# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Tuntuɓar juna tsakanin addinai: Haɗin kan mutanen Sodangi
## Kashi na takwas: An ga samu, an ga rashi


Wanda ya rubuta: Romie Singh
Wanda ya tace: Katrin Ogunsade, Naïma Guira
Wanda ya fassara: Ɗanlami Bala Gwammaja


**'Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| Nas Rakiya: | 'yar shekara 28 |
| Hassan: | ɗan shekara 12, ƙanen Layla |
| Fada Bana: | ɗan shekara 49, kawun Dauda |
| Dauda: | ɗan shekara 17 |
| Layla: | 'yar shekara 16 |
| Saima: | 'yar shekara 16 |
| Ɗanjuma: | ɗan shekara 17 |
| Maryam: | 'yar shekara 16 |
| Tafida: | ɗan shekara 17 |

**MAI GABATARWA:**

Masu sauraronmu, barkanmu da sake saduwa da ku a cikin shirinmu na "Ji Ka Karu" mai taken "Haɗin kan mutanen Sodangi", wanda a cikinsa za ku ji yadda addini da siyasa suka haddasa zaman doya da man ja a tsakanin al'ummomi guda biyu, da kuma wasu maƙwabtan juna su biyu, da kuma tsakanin wasu matasa guda biyu, Dauda da Layla. A shirin namu na yau mai suna "An ga samu, an ga rashi" za mu ji yadda halin Hassan ya sauya, sannan kuma mu ji ko Dauda ya faɗa tarkon da Tafida ya kafa masa.

**Fitowa ta 1: A asibiti**

Hassan, Nas Rakiya

**NAS RAKIYA:** Sannu Hassan, yaya jiki? Tashi ga abinci na kawo maka.

**HASSAN:** Yauwa, Nas Rakiya. Yau jikin nawa da sauƙi sosai. Uhmm... don Allah in tambaye ki wani abu mana game da addininku.

**NAS RAKIYA:** Tambayi mana, ba kome!

**HASSAN:** Me ya sa na ji jiya kina cewa ku Yahudawa ne 'yan ƙabilar *Lemba*?

**NAS RAKIYA:** Gaskiya ne. Wato kamar kimanin shekaru dubu biyu da suka wuce, an samu cewa akwai ƙabilu guda goma a daular Isra'ila, waɗanda aka tarwatsa su, suka yi gudun hijira. Sai suka zauna a wuraren da yanzu ake kira da suna Iraƙi da kuma Syria. Daga nan kuma sai suka watsu zuwa Kudu wajejen ƙasar Habasha. Bari ma ka ga in nuna maka yadda abin yake a cikin taswirar da na zo maka da ita.

**HASSAN:** Haka suka sha tafiya har zuwa gabashin Afirka?

**NAS RAKIYA:** Muna zaton haka. Kalli ka ga yadda gine-ginen ƙasar Zimbabwe suke a da. Mu 'yan ƙabilar Lemba, muna ganin cewa kakanninmu ne suka fara gina wannan tsohon gari. Sai dai kuma ka san akwai jinsunan Yahudawa a ko'ina cikin yankunan gabashi da yammacin Afirka.

**HASSAN:** Ai kuma kin ce su 'yan ƙabilar *Lemba* suna da al'adu irin na Yahudawa. Me kike nufi?

**NAS RAKIYA:** Haka ne. Abin da nake nufi shi ne, cewa Musulmi da Yahudawa duk daga tsatso ɗaya suka fito. Wato dukkaninsu Annabi Ibrahim shi ne kakansu, ko da kuwa su Yahudawa suna danganta kansu da ƙasar Israi'ila, ko kuma su Musulmi suna danganta kansu da ƙasar Makka ko Madina. Kai wasu bayanan ma suna nuna cewa kome nasu iri ɗaya ne. Misali, ku Musulmi kuna kiran naman da kuke ci *halal*, ko ba haka ba? Mu kuma namu *kosher* muke kiransa, wato yana nufin duk dabbar da aka yanka da sunan Allah. Mu ma 'yan ƙabilar *Lemba* haka muke yanka dabbobinmu. Ku Musulmi ba kwa cin naman alade, mu ma ba ma ci. Ina fata ka gane?

**HASSAN:** Kin san wani abu kuwa, Nas Rakiya?

**NAS RAKIYA:** Me fa Hassan?

**HASSAN:** Ko za ki iya kawo min ziyara idan an sallame ni na koma gida?

**NAS RAKIYA:** Haba Hassan, zan zo ma ni da 'yata. Sai na in nemi izini wajen babanka don na ɗauke ka mu fita ganin gari a ƙarshen mako.

**HASSAN:** Yaya sunan 'yar taki?

**NAS RAKIYA:** Rifkatu. Nan da wata mai kamawa za ta cika wata goma.

**HASSAN:** To, don Allah ku sallame ni gobe mana!

**NAS RAKIYA:** Me zai hana. Ga shi ma ƙunan da ke hannunka ya fara warkewa. Ai kana samun sauƙi sosai, mutumina! Yanzu mai da hankali ka ci abincinka.

**MAI BA DA LABARI:**
Shi kam Hassan bai san tsaka-mai-wuyar da yake ciki ba. Tuni da ma Fada Bana ya riga ya shigar da ƙara a babban ofishin 'yan sanda na Sodangi a kan sa wutar da aka yi wa cocinsa. Shi dai Hassan bai san abin da ake ciki ba. Amma kuma Dauda ya san kome. Don haka ne ma ya zo yanzu don ya rarrashi kawun nasa a kan maganar. Yanzu dai ga su nan a zaune a cikin wannan coci.

**Fitowa ta 2: A coci**
Fada Bana, Dauda

**FADA BANA:** Wannan aljanin yaron bai ma san yadda zai cinna wuta a cocin ba, sai ya ɓige da ƙona kansa!

**DAUDA:** Wannan aljanin yaron da kake magana a kansa shekararsa goma sha biyu kacal. Kuma cikin 'yan watannin nan mahaifiyarsa ta mutu. Shi kamar sojan bante yake kawai. Ka san cusa masa ra'ayi aka yi.

**FADA BANA:** A'a! Wai kai Dauda, me ya sa kake ta kare shi ne? To, ai na san dalili, wato don kawai kana son yayarsa ne Layla. Gaskiya bari in gaya maka, ni ba abin da zan iya yi maka a kai. Wato a maimakon ka mayar da hankalinka don ka zamo

fada, ka gwammace ka ɓata lokacinka wajen kare waɗannan mutanen da ba masu bi ba.

**DAUDA:** Haka ne? Wato su su ne waɗanda ba masu bi ba, mu kuma mu ne kafirai! Kai! Ba dai daɗi irin waɗannan sunayen da muke kiran juna da su! Ni dai Kawu, so nake ka gane cewa na san Hassan ya tabka kuskure, amma a matsayinka na Kirista, an san ka da tausayi da afuwa. Jininka fa na son 'yan'uwa ne a matsayinka na ɗan Sodangi, haka kuma an san ka da mutunta mutane.

**FADA BANA:** Ka ga, harkar nan fa akwai siyasa a cikinta. Maganar ba wai a kan Hassan kawai take ba. Abin da muke so kawai shi ne kada Kungiyar Musulmi ta gina masallacinta a wannan fili. Mu so muke mu gina babbar coci a cikinsa. Ni yanzu ma wannan harin da aka kai wa cocin tamu ya taimaka wa wannan fafutuka da nake. Har ma Rabaran Haruna Emah ya yi alƙawarin bayar da gudummawar dala dubu goma. Idan kuwa har ya dafa mana, to lalle za mu yi rinjaye a Majalisar Hukumar Raya Birane. Za mu iya cinye ƙuri'ar majalisar cikin sauƙi, kuma mu yi galaba.

**DAUDA:** Wato yanzu kai so kake ka haɗa kanka da wannan da yake kiran kansa Rabaran. Kawu, ina so ka gane cewa wannan mutumin fa macuci ne. Zaluntar talakawa kawai yake!

**FADA BANA:** Kai Dauda, tafi ka ji da shugabancin ɗaliban da kake kawai, ni ka bar ni na ji da wannan al'amarin. Idan kuma ka ga ba za ka damu ba, lokacin addu'ar maraice ya yi, sai ka tsaya mu yi, ko ka ji dan dama-dama.

**DAUDA:** Ni kuwa lalle zan yi addu'ar Ubangiji ya canza maka ra'ayinka, Kawu!

**MAI BA DA LABARI:**
Yanzu dai hankalin Dauda a kwance yake a makaranta. Ita kuma Layla ta komo makarantar bayan ta gama jiyyar ƙanenta Hassan a asibiti! Yanzu babansa ne, Malam Isma'ila Umar, ke kula da shi a gida. Shi kuma Tafida yana sa ran shi da Layla da Maryam za su hađu a wani zaman da Kungiyar Muhawara za ta yi da ƙarfe uku na yamma. Yana ganin wannan lokacin shi ya fi dacewa na aiwatar da abin da ya shirya.

**Fitowa ta 3: A Kungiyar Muhawara**
Layla, Dauda, Đanjuma, Saima, Maryam

**LAYLA:** Ya isa, don Allah kowa ya yi shiru! Ina miƙa godiyata ga Maryam, da ta kama min aikina a Kungiyar Muhawara a lokacin da ba na nan. Haka kuma ina miƙa godiyata gare ku duka, da kuka sami damar halartar wannan zaman. A yau batun da yake gabanmu shi ne: Me ya sa ake samun cewa 'yammata ba sa ƙaunar darussan lissafi da na kimiyya? Yauwa Saima, me za ki ce?

**SAIMA:** Ni a gaskiya ina son na dinga fahimtar lissafi, amma shi wani irin darasi ne da nake jinsa kamar wani yare na dabam. Wataƙila yadda ake koya mana shi ne yake kawo matsalar.

**ĐANJUMA:** Gaskiya ma dai har da tasirin wurin da mutum yake da zama. Kun ga ai a ƙasashen China da Rasha ana ƙarfafa wa mata gwiwa su dinga đaukar darussan lissafi da na kimiyya.

**MARYAM:** Wannan haka yake, Đanjuma. Wađannan ƙasashen da ka fađa, su ne wuraren da wađanda ba su yarda akwai Ubangiji ba suka ci nasarar murƙushe addinai. … Ku tsaya! Ina ganin

cewa ilimin kimiyya fa ya cika haɗari, musamman ganin yadda yake ƙaryata Littafi Mai Tsarki!

**ƊANJUMA:** Gaskiya Maryam, ba haka ba ne. Kimiyya fa tsagwaron ilimi ne tsantsa. Kuma duk mai ilimin kimiyya ba abin da yake illa ya yi bayani a kan abubuwan da yakan lura da su a muhallin da yake.

**MARYAM:** Ni amsar da zan ba ka ita ce: Ubangiji yana ko'ina. Mutane sun ƙirƙiro ilimin kimiyya ne kawai don su raba mu da Ubangiji.

**DAUDA:** Bari in tuna muku da wani abu. Kun san fa masanin kimiyyar nan ɗan ƙasar Birtaniya da ake kira Charles Darwin, wanda mutane suke ta danganta shi da abin tsiya, to ai ma'abocin zuwa coci ne a lokacin da ya taso yana matashinsa. Haka kuma shi mutum ne mai zurfin tunani, da kuma lura da abubuwa. Ya yi tafiye-tafiye da dama kuma ya ga halittu dabam-dabam, kuma ya ga ya dace ya yi wa mutane bayanin yadda rayuwar waɗannan halittu take. Za a iya cewa Ubangiji ne ya ba shi damar nemo bayanai a kan abin, har ta sa ma ya rubuta littafinsa da ake kira *"The Origin of Species",* mai bayani a kan asalin halittu.

**ƊALIBAI:** *Wow!* Gaskiya. Kai! Amma ya yi ƙoƙari!...

**MAI BA DA LABARI:**
A yayin da ake ta tafka wannan muhawara, sai Tafida ya lallaɓa ya ajiye sarkar nan ta kuros, da Maryam ta ba wa Dauda wadda shi kuma a yanzu haka take hannuna, a tsakanin Dauda da Layla. To, yanzu an gama wannan zama na Kungiyar Muhawarar. Fatana shi ne Layla ta ga wannan sarƙa da ya ajiye. Kuma hakan aka yi, don kuwa ta gani!

**Fitowa ta 4: A makaranta**

Layla, Tafida, Dauda

**LAYLA:** A'a! Mene ne wannan haka?

**TAFIDA:** Kai, kai, kai! Ai sarƙar gwal ce mai kuros. Taka ce Dauda?

**DAUDA:** Me fa? Au…

**LAYLA:** Dauda, wannan taka ce? Ko kawunka ne ya ba ka ita?

**DAUDA:** Uhmm…a'a…uhmm… Gaskiya dai Maryam ce ta ba ni.

**LAYLA:** Maryam kuma, Dauda? Saboda me ta ba ka? Shi ne kuma kake sanye da ita, bayan ka san cewa an hana sa kaya masu nuna addini a wannan makarantar?

**DAUDA:** Ni ba sa ta na yi ba. Ni ban ma san yadda aka yi na gan ta a nan ba. Ni…ni…

**LAYLA:** Haka ne. Yanzu na fahimci kome! Ni lokaci ma ya yi, gida zan tafi. Sai gobenku.

**MAI BA DA LABARI:**

Kamata ya yi a ce Dauda ya yi wata 'yar ƙarya a wannan lokaci. Sai dai kuma shi mutum ne mai gaskiya. Amma dai abin ya girgiza Layla. Tafida kuwa a ɓangarensa sai ya ga dama ta samu, don kuwa nan take sai ya yunƙura!

**TAFIDA:** Layla, Layla! Zo in ɗan raka ki gida mana!

**LAYLA:** To, Tafida, wallahi ka kyauta! Ka sa na ji daɗi! Don Allah raka ni gidan.

**MAI BA DA LABARI:**

Tafida ya ɗauka zai ji kamar wanda ya yi tsintuwa, amma kuma da suka jera da Layla sai ya ji kuma duk kunya ta kama shi. Bayan sun yi sallama da ita, sai ya wuce gida. Sam bai ji daɗi ba. Kwatsam sai idonsa ya kai kan wani hoto da ke kan teburin babansa. Hoton na wata mata ce kyakkyawa, tana ɗauke da ɗan jinjiri a hannunta. Fuskarta ta ja hankalinsa, amma bai san dalili ba. Ya kamata a ce ya tambayi wani ya gaya mishi wace ce ita.

**MAI GABATARWA:**

To, yau kuma a nan za mu ja linzamin shirin namu na "Ji Ka Karu" a kan "Haɗin Kan Mutanen Sodangi". Ku biyo mu a shiri na gaba domin jin ko Dauda da Layla sun sami galabar jawo hankulan iyayensu don su sulhunta. Kafin nan kuna iya ziyartar adireshinmu na yanar gizo, wato www.dw-world.de/lbe, domin sake jin shirin ko kuma aiko da tsokaci.